السنّة النبوية وعلومها
www.sunnah.global

# Imanin ɗayanku ba ya cika har sai na kasance mafi soyuwa a gare shi sama da babansa da 'ya'yansa da mutane bakiɗaya

An karbo daga Anas Allah Ya yarda da shi, ya ce: Ma'aikin Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: Imanin ɗayanku ba ya cika har sai na kasance mafi soyuwa a gare shi sama da babansa da 'ya'yansa da mutane bakiɗaya.
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana ba mu labarin Musulmi ba zai kasance mai cikakken imani ba har sai ya gabatar da son Ma'aikin Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, a kan son babarsa da babansa da ɗansa da 'yarsa da mutane bakiɗaya, wannan soyayya kuwa tana hukunta yi masa biyayya da taimaka masa da kuma barin saɓa masa.

https://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/5953

النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee